# Littafi mai Tsarki na yara

**Ke gabatar da**



# Kyakkyawan Wawan Sarki


**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Janie Forest**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: Lyn Doerksen**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**



**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**



**©2024 Bible for Children, Inc.**
Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan har ba zaku sayar da shi.




**Sama'ila, alkali da shugaban Isra'ila yanzu ya tsufa. Ya mai da 'ya'yansa alkalai a kan Isra'ila, domin su dauki matsayinsa a hidimar Allah. Amma 'ya'yan Sama'ila sun kasance da mugunta. Suna son kudi suna kuma amfani da iko domin samun kudi cikin rashin gaskiya.**



Mutanen Isra’ila sun sha wahala saboda muguntan ‘ya’yan. Babu gaskiya a wuraren shari’a. Duk lokacin da mutanen suna neman taimako daga ‘ya’yan Sama’ila dole sai sun biya.



3

Dole sai an yi wani abu. Wata rana, dattawan Isra’ila suka taru suka kuma roka Sama’ila ya taimake su.



4

“Ka ba mu Sarki ya yi mana shari’a,” dattawan suka bukata. Ba su so mugayen ‘ya’yan Sama’ila su yi musu shari’a. Sun bukaci sarki daidai da sauran al’umman da suke kewaye da su.



5

Sama’ila ya yi fushi. Isra’ila ta riga ta samu Sarki! Allah Maidukka, Madawwami, wanda yake mulki a kan Isra’ila. Tun da, ya riga ya ‘yantar da su daga bauta a Masar, ya bude Teku mai ciyawar iwa domin su kubce.

6



Sa’an nan ya ba wa Isra’ila kasa mai kyau.

7

Sa’ad da Sama’ila ya yi addu’a, UBANGIJI ya ce, “Ba su kii ka ba, amma ni ne suka kii, domin kada in yi mulki a kansu. Sun yi wa wadansu alloli hidima. Ka saurare muryoyinsu ka ba su sarki.”



8


Allah ya gaya wa Sama'ila ya gargadi mutanen cewa sarkinsu na duniya zai kwace kudinsu a haraji; zai taimake kansa a filayensu mafi kyau da gonakin inabinsu; zai umarta 'ya'yansu su shiga aikin soja nasa; ya umarta 'ya'yansu mata su yi masa aiki.
9


GONAR INABI NA MASARAUTA
Amma mutanen sun so a ba su sarki kawai.
Kada a yi kusa
10


Allah ya bi da Sama'ila zuwa wurin wani kyakkyawan saurayi, mai kunya, mai TSAYI sosai – kansa ya fi kowa tsayi. Sunansa Shawulu. Sa'ad da Sama'ila ya ga Shawulu, UBANGIJI ya ce, "Wannan zai yi mulki a kan mutane na."
11


Cikin biyayya, Sama'ila ya shafe Shawulu ya zama sarkin Isra'ila. Sa'ad da ya mika Shawulu ga mutanen Isra'ila, sai suka yi ihu, "Ran Sarki Ya Dadde!"
12


Ba a dadde ba sai aka gwada Sarki Shawulu. Ammonawa, wadanda sun ki jinin Isra'ila, suka kewaye birnin Isra'ilawa suna barazanna yaki domin su ciccire idon dama na kowane namiji. Wani mugun shiri! Labarin barazanan ya kai kunnen Sarki Shawulu. Sai ya shirya sojojinsa.
13


Sa'ad da rundunar sojoji biyun suka sadu, Shawulu ya hallakar da Ammonawan ya kubutar da birnin. Sarki Shawulu ya ba wa Allah daukakar, yana cewa "… yau UBANGIJI ya cika ceto a Isra'ila!"
14

Allah ya ba Shawulu babban nasara a ranar. Amma ba kullum ba ne Shawaulu yana daukaka Allah. Wata rana, kafin ya yi yaki da Filsitiyawa, Shawulu ya mika hadaya ga Allah. Ya sani cewa wannan aikin hannun Sama'ila ne. Ya sani cewa Allah yana so ya jira sai Sama'ila ya zo ya yi hadayan. Amma Shawulu ya yi rashin biyayya ga Allah.



15

Sa'ad da Sama'ila ya iso, sai ya ce wa Shawulu, "Ka yi wawanci. Ba ka kiyaye dokan UBANGIJI Allahn ka ba. Yanzu mulkinka ba zai ci gaba ba."



16

Watakila Shawulu yana zato abinda ya yi karamin zunubi ne. Amma rashin biyayya ga Allah ba karamin abu ba ne.



17

Wani lokaci kuma, Allah ya ba wa Shawulu oda ya halakar da mugayen mutanen Amalek.



Amma Shawulu da mutanen suka bar Sarki Agag na Amalek ya rayu. Sun kwashe ganima suka ajiye, raguna da awaki. Shawulu ya ce sun ajiye kayan ne domin mika hadaya ga UBANGIJI.

18



Sama'ila ya gaya wa Shawulu, "Yin biyayya ya fi hadaya. Ka ki kalmar UBANGIJI, UBANGIJI kuma ya ki ka daga zama sarki a kan Isra'ila." Shawulu ya tuba daga zunubinsa. Amma lokaci ya riga ya wuce. Sauran kwanakin ransa sun kasance da bakin ciki saboda ya ki ya yi biyayya ga UBANGIJI.

19

Kyakkyawan Wawan Sarki

Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki

a na samu a

1 Sama'ila 8-16

"Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske." Zabura 119:130

20






**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**